# Kungiyar **"Neman Gaskiya"**

BABI 1
DARASI 1:




Kafin ka fara: Ga darasi na fari cikin takwas wadanda za ka iya samu ban da biyan kudi, daga masu aika maka su.

Abin da za ka yi kawai:

1. Ka karanta darasin
2. Ka cika takarda ta tambayoyi
3. Ka aiko mamu ita.

Mu kuma za mu duba takarda, mu rubuta kome daidai, mu maida maka ita in akwai wani kuskure don a gyara, sa'a nan mu aika darasi maibiyarta. In ka gama darasin nan 8, za mu ba ka certificat mai kyau da sunanka gare shi.

## Kashi na ɗaya: YAYA ALLAH SHI KE?

Gaisuwa da fatan alheri.




Bayan haka wannan darasi yana magana game da Allah.

Ko ka taɓa yin tambaya cewa yaya Allah shi ke? Lalle girman Allah da ban mamaki nashi sun wuce tunaninmu. Ba za mu iya saninsa sarai ba. Duk da haka Allah ya ba mu Littafi mai kyau ainun wanda ya ke magana game da Shi. Wannan littafi Littafi Mai Tsarki ne, Maganar Allah ke nan. Allah ya halicci rana da wata. Ya halicci dukan tamrari waɗanda ke bisa gare mu; ba su lissaftuwa! Allah

ya halicci duniya, ya halicce mu kuma. Littafi Mai Tsarki yana nuna wasu abubuwa da yawa game da Allah.

# Allah Mai Iko Duka ne

ALLAH MAI IKO DUKA NE. Watau Allah da ikonsa yana mulkin dukan kome. Ba abin da bai iya yi ba. Ba abin da ya buwaye shi! Littafi Mai Tsarki ya ce: "Ai, ba abin da zai gagari Allah yi." Luka 1:37.

Allah yana da ikon kome. In an kwatanta shi da sarakunan duniya, za a ce lalle su duka ba su da ikon kome. Allah ya iya yin kome da shi ke so shi yi.

# Allah Ruhu ne

ALLAH RUHU NE. Ko ka taɓa tunanin dalilin da mutum ba shi iya ganin Allah? Dalili ke nan, Allah Ruhu ne, kuma ba a ganin Ruhu. Lokacin da Allah ya yi mu, ya ba mu jiki, amma kuma ya sa ruhu mai rayuwa cikin jikinmu. Mutane suna ganin jikunanmu, amma ba dama su ga ruhunmu.

Allah dai Ruhu ne gaba ɗaya! Ba shi da jiki irin namu, shi ne dalilin da ba mu iya ganinsa. Littafi Mai Tsarki ya ce: "Allah Ruhu ne, masu yi masa sujada kuma sai su yi masa sujada cikin ruhu da cikin gaskiya kuma."

Ko da shi ke ba mu iya ganin Allah ba, mun iya mu san shi, mu ƙamnace shi. Sanin Allah ya fi kome muhimmanci cikin duniya. Idan mun san Allah, lalle za mu iya zama da murna sosai. In mun san Allah za mu ƙamnace Shi mu dangana gare shi, mu yi masa sujada.

# Allah Mafi Ɗaukaka ne

ALLAH MAFI ƊAUKAKA NE. Hasken ɗaukakar Allah yana walƙiya har ba dama mu duba shi. Ko hasken rana idanunmu ba su iya dubawa, sai idanu su yi ciwo. In mutum ya daɗe yana kallon sama zai makamce. Ɗaukakar Allah ta fi walƙiyar hasken rana ainun. Dalili ke nan da ba mu iya duban ɗaukakarsa ba. Allah ya ce, "Mutum ba shi ganina shi rayu." (Fitowa 33:20)



Littafi Mai Tsarki ya ba mu labarin wani mutum mai suna Musa. Wannan mutum aboki zaɓaɓɓe ne na Allah. Allah ya yi magana da shi sau da yawa. Duk da haka, Musa bai taɓa ganin Allah ba. Wata rana Musa ya roƙi Allah shi yi wani abu dabam. Ya ce ma Allah, "Ina roƙonka, ka nuna mani darajarka." Allah ya amsa masa cewa, "Ba ka da iko ka ga fuskata, gama mutum ba shi ganina shi rayu. Ubangiji Ya ce, "Ga wani wuri kusa da ni inda za ka tsaya a bisa wani dutse. Za ya zama kuma sa'anda darajata tana giftawa, zan sanya ka cikin tsaguwar dutse, in rufe ka da hannuna har na wuce." (Fitowa 33:20-22).

To, Musa ya hau bisa dutse. Allah kuma ya ɓoye shi cikin tsaguwar dutsen. Sa'a nan Allah ya sa hasken ɗaukakarshi ya bi gaban idanun Musa. Musa bai ga fuskar Allah ba, amma hasken nan kaɗan da ya gani ya mai da fuskarshi ta haskaka da walƙiya kamar rana! Lokacin da Musa ya sabka daga dutsen, wannan walƙiya ta fuskarsa ta ba mutane tsoro. Ba abin mamaki ne ba,

Musa da mutanensa suka yabi Allah da babbar murya, cewa , "Wanene ya yi kama da kai, ya Ubangiji; Wanene kamarka, maɗaukaki cikin tsarki?" (Fitowa 15:11)

# Allah Mai Tsarki ne

ALLAH MAI TSARKI NE: Watau Allah yana da tsabtaccen hali ainun, kamili ne, ban da zunubi. A cikinsa babu aibi ko ɗaya.

Wanibi Littafi Mai Tsarki yana aiki da maganar 'duhu' in yana nufin zunubi. Game da halin Allah Maɗaukaki ya ce, "Allah haske ne, a cikinsa babu duhu (watau zunubi) ko kaɗan."

Allah haske ne duk, mai ɗaukaka ne duk. Shi mai tsarki ne, ba shi da zunubi, kullum yana aiki da nagarta da adalci. Babu ƙazamta ko rashin tsabta da zai kasance wajensa. Littafi Mai Tsarki ya ce: "Gama Ubangiji Allahnmu Mai Tsarki ne." (Zabura 99:9)

Wata rana Allah ya yi magana da wani annabi mai suna Ishaya cikin ru'ya. Ru'ya kamar mafalki ne. Cikin ru'ya, annabi Ishaya ya ga Allah yana bisa kursiyinsa. Mala'iku dubun dubbai suna kewaye da shi suna yabon Allah suna cewa, "Mai-tsarki, Mai-tsarki, Mai-tsarki ne, Ubangiji mai runduna: dukan duniya cike ta ke da ɗaukakarsa." Da Ishaya ya ga wannan ru'ya ta Ubangiji Allah ya ji tsoro. Ru'yan nan ta nuna masa shi mai zunubi ne, Allah kwa Mai Tsarki ne.



# Allah Kamna ne

ALLAH KAMNA NE: Watau Ubangiji Allah yana ƙamnarmu, yana so ya ba mu abin da zai amfane mu kawai. Ko da shi ke shi Ubangiji mai iko duka ne na sama da ƙasa, ya san kowane ɗayanmu; yana ƙamnar kowane ɗayanmu kuma. Ya san ka, ya san ki, yana ƙamnarka, yana ƙamnarki.

Ya yiwu za ka ce, "To ƙaƙa zan sani Allah yana ƙamnata?" Ga hanya biyu inda za ka tabbata Allah ya ƙamnace mu.

1) MUN SANI ALLAH YANA KAMNARMU SABODA YA FAƊA MAMU HAKANAN. Allah ya ce cikin Maganarsa: "Hakika na yi ƙamnarka da madawamiyar ƙamna." (Irmiya 31:3)

2) MUN SANI ALLAH YANA KAMNARMU SABODA YA BA DA ƊANSA YA MUTU DOMINMU. Littafi Mai Tsarki ya ce: "Allah yana shaidar ƙamnatasa garemu, da shi ke, tun muna masu-zunubi tukuna, Kristi ya mutu sabili da mu." (Romawa 5:8)

Mutane da yawa suna tsammani Allah ba ya sonsu saboda sun yi miyagun ayyuka, sun yi magana mara kyau kuma. Gaskiya ne, Allah yana ƙin zunubi, amma bai ƙi mu mutane ba. A'a, Yana ƙamnarmu, har ya shirya wata hanya inda mun iya mu karɓi gafarar zunubanmu. Maganar Allah ta ce,

> "Allah ya yi ƙamnar duniya, har ya ba da Makaɗaicin Ɗansa, domin dukan wanda ya ba da gaskiya gare shi kada ya halaka, amma ya sami rai na har abada." (Yohanna 3:16)


Wannan aya ta nuna mamu Allah ya ƙamnace mu, da kai da ke, da ni, har ya ba da tilon Ɗansa, Ubangiji Yesu Almasihu, don ya mutu bisa gungumin itace (gicciye) saboda zunubanmu. Lokacin da muka karɓe shi ya zama Mai Cetonmu, Allah yana gafarta mamu dukan zunubanmu, yana maishe mu 'ya'yansa. Saboda haka, muna da rai na har abada. Tun da Allah ya

ƙamnace mu da yawa haka, yana so mu kuma mu ƙamnace shi. Littafi Mai Tsarki ya ce; “Ka ƙaunaci Ubangiji Allahnka da dukan zuciyarka, da dukan ranka, da dukan hankalinka.” (Matiyu 22:37)

Allah yana murna in mun sa zuciya mu ƙamnace shi da zuciya duka. Littafi Mai Tsarki ya bayyana yadda Sarki Dauda yake babban mutumin Allah. Ga abin da Dawuda ya ce: “Ina ƙamnarka, ya Ubangiji, ƙarfina.” (Zabura 18:1) Waɗannan maganganu sun faranta ma Allah rai sosai. Allah zai yi murna in ka zaɓe shi kana ƙamnarsa kamar yadda Dawuda ya ƙamnace Shi. Ga wata addu’a mai taimakonka:

“Ya Ubangiji, lalle ina so in yi ƙamnarka da dukan zuciyata! Ka taimake ni in ƙara saninka. Na gode don ka aiko Ɗanka, Ubangiji Yesu, ya mutu bisa giciye domin zunubaina, ya tashi da rai kuma.”

## AYA TA HADDACEWA:




Copyright © 2004 The Mailbox Club Int’l Inc.
All rights reserved. Used by permission.





Domin ku sami arziki, sai ku yi anfani da asiri na ƙasa domin ku tone ɓoyayyun baƙaƙe

| | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|
| ◘ A | ⟡ C | ● D | ▣ H | ◇ I | ⊡ K | |
| ○ Ƙ | ⧈ L | ⟐ N | ◉ R | ■ U | ◈ Y | □ Z |

⊡ ◘   ○ ◘ ■ ⟐ ◘ ⟡ ◇

__ __   __ __ __ __ __ __ __



◘ ⧈ ⧈ ◘ ▣   ● ◘

__ __ __ __ __   __ __

● ■ ⊡ ◘ ⟐   □ ■ ⟡ ◇ ◈ ◘ ◉ ⊡ ◘

__ __ __ __ __   __ __ __  __ __  __ __ __ __

# TAMBAYOYI DOMIN DARASI 1

Sai ku zaɓi amsar da ta fi zama daidai (‘a’ ko ‘b’), ka rubuta ga filin da ke nan.

Kwatanci: [b] a) A sama akwai zunubi kaɗan
b) A sama babu zunubi ko kaɗan

1. Littafi Mai Tsarki ya ce Allah mai iko duka ne. Me ya nufa?
   ☐ a) Allah yana da iko da yawa na sama da ƙasa.
   b) Allah yana da iko duka na sama da ƙasa.
2. Ba mu ganin Allah saboda
   ☐ a) Allah ruhu ne, ba a iya ganin ruhu.
   b) Allah yana da nisa ƙwarai, har ba a iya ganinsa.
3. Littafi Mai Tsarki ya ce Allah mai Tsarki ne. Me ya nufa?
   ☐ a) Allah yana da hali mai kyau.
   b) Allah mara aibi ne, kamili ne, ba shi da zunubi.
4. Mun iya sanin Allah yana ƙamnarmu saboda
   ☐ a) Mutane suna cewa ya ƙamnace mu.
   b) Littafi Mai Tsarki ya faɗa mamu haka.
5. Mun sani Allah yana ƙamnarmu saboda
   ☐ a) Ya ba da Ɗansa ya mutu domin zunubanmu.
   b) Muna ji kamar yana ƙamnarmu.

Ka rubuta ayar haddacewa nan:

Ka rubuta nan “Arzikin” da ka samu

Rubuta sunanka da na babanka

Shekarunka nawa?

In kana cikin makaranta, wane aji?

Sunan garinku